# SŨRATUL 'ALAƘ سُورَةُ العَلَقِ

Tana karantar da cẽwa karãtu shi ne gaba da kõme, amma a gama shi da sũnan Allah, kuma a yi aiki da shi dõmin a sãmi kiyãyewar Allah daga dukan maƙiyin addĩni.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, wanda Ya yi halitta.

*2.* Ya halitta mutum daga gudan jini.

*3.* Ka yi karatu, kuma Ubangijinka Shi ne Mafi karimci.

*4.* Wanda Ya sanar (da mutum) game da alƙalami

*5.* Ya sanar da mutum abin da bai sani ba.

*6.* A'aha! Lalle, ne mutum, haƙiƙa, yana girman kai (ya ƙi karatu).

*7.* Dõmin yã ga kansa, yã wadãta.

*8.* Lalle ne zuwa ga Ubangijinka makoma take,

*9.* Shin, kã ga wanda ke hana,

*10.* Bãwã idan yã yi salla?

*11.* Ashe, kã gani, idan (shi bãwan) ya kasance a kan shiriya?

*12.* Ko ya yi umurni da taƙawa?

ٱقْرَأْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلَّذِى خَلَقَ ﴿١﴾

خَلَقَ ٱلْإِنسَٰنَ مِنْ عَلَقٍ ﴿٢﴾

ٱقْرَأْ وَرَبُّكَ ٱلْأَكْرَمُ ﴿٣﴾

ٱلَّذِى عَلَّمَ بِٱلْقَلَمِ ﴿٤﴾

عَلَّمَ ٱلْإِنسَٰنَ مَا لَمْ يَعْلَمْ ﴿٥﴾

كَلَّآ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَيَطْغَىٰٓ ﴿٦﴾

أَن رَّءَاهُ ٱسْتَغْنَىٰٓ ﴿٧﴾

إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلرُّجْعَىٰٓ ﴿٨﴾

أَرَءَيْتَ ٱلَّذِى يَنْهَىٰ ﴿٩﴾

عَبْدًا إِذَا صَلَّىٰٓ ﴿١٠﴾

أَرَءَيْتَ إِن كَانَ عَلَى ٱلْهُدَىٰٓ ﴿١١﴾

أَوْ أَمَرَ بِٱلتَّقْوَىٰٓ ﴿١٢﴾

*13.* Ashe, kã gani, idan (shi mai hanin) ya ƙaryata, kuma ya jũya bãya?

أَرَءَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ﴿١٣﴾

*14.* Ashe, bai sani ba cewa Allah Yanã gani?

أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ﴿١٤﴾

*15.* A'aha! Lalle ne idan bai hanu ba, lalle ne zã Mu ja gãshin makwarkwaɗa

كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ لَنَسْفَعًۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ﴿١٥﴾

*16.* Makwarkwaɗa maƙarya-ciya, mai laifi.

نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ﴿١٦﴾

*17.* Sai ya kirayi ƙungiyarsa.

فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ﴿١٧﴾

*18.* Zã Mu kirayi Zabaniyãwa (mala'iku mãsu girma).

سَنَدْعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ﴿١٨﴾

*19.* A'aha, kada ka bĩ shi. Kuma ka yi tawali'u,(1) kuma ka nemi kusanta (zuwa ga Ubangijinka).

كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَٱسْجُدْ وَٱقْتَرِب ۩ ﴿١٩﴾

## SŨRATUL KADR سُورَةُ القَدْرِ

Tana karantar da son Allah ga wannan al'umma ta Musulmi, da Ya ba su Lailatul Ƙadari dõmin Ya yawaita ladar ayyukansu ko da yake rãyukansu bã su da tsawo kamar na al'ummomin farko.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Lalle ne Mũ, Mun saukar da shi (Alƙur'ãni) a cikin Lailatul Ƙa-dari (daren daraja)

إِنَّآ أَنزَلْنَٰهُ فِى لَيْلَةِ ٱلْقَدْرِ ﴿١﴾

---

(1) Wato salla da sauran ibãdodi.